DAGA CIKIN LADUBBAN AZUMI DA SUNNONINSA:

KUMA BAYAN YA BUDA BAKI YANA CEWA:: “KISHIRWA TA TAFI JIJIYOYI SUN JIKU KUMA LADA YA TABBATA, INSHA ALLAH. ”[HADISIN HASSAN NE – [ABU DAWOOD NE YA RUWAITO SHI].

• NESANTAR KWARKWASA; KWARKWASA IT ACE WAUTA, DA KUMA MAGANGANUN BANZA.

• DAGA CIKIN ABABEN DA KE TAFIYAR DA KYAWAWAN AYYUKA, YIN ABABE MARASA KYAU DA SHAGALA INTERNET, DA FINA-FINAI, DA KALLON WASANNI, DA ZAMAN KAN HANYOYI DA GANTALI A GARI.

• KADA A WUCE GONA DA IRI;WAJEN CIN ABINCI, SABODA HADISIN DA KE CEWA: “DAN`ADAM BAI TABA CIKA WANI MAZUBI MAFI SHARRI BA SAMA DA CIKINSA” [- HADISIN SAHIHI NE TIRMIZI NE YA RUWAITO SHI.]

KYAUTAR ABINCI, KUDI, KYAUTATAWA MAKOTA, YIN AIKIN KIRKI DA JIKI DA NAGARTATTUN HALAYE. MANZON ALLAH (S.A.W) YA KASANCE YAFI KOWA KYAUTA, AMMA SANDA YAFI KOWANE LOKACIN YIN KYAUTA SHI NEA CIKIN WATAN RAMADAN. [BUKHARI DA MUSLIM NE YA RUWAITO SHI].

DAGA CIKIN ABIN DA YA KAMATA A AIKATA A WANNAN WATAN MAI GIRMA:

SAMAR DA YANAYI DA SHIRYA KAI DOMIN YIN IBADA, DA GAGGAUTA TUBA. DA KUSANTAR ALLAH, DA MURNAR SHIGA WATAN RAMADAN, DA INGANTA

AZUMI, DA TSORON ALLAH A WAJEN SALLAR DARE, DA RASHIN GAJIYA A DA. AL-WASIT, DAREN LAILATUL KADARI, DA SADAKA, DA ITTIKAFI.

• BABU LAIFI ZAMU IYA TAYA JUNA MURNAR SHIGAR WATAN, HAKIKA MANZON ALLAH (S.A.W) YA KASANCE YANA YIWA SAHABBANSA BASHARA DA WATAN RAMADHAN, KUMA YANA KWADAITAR DASU DA SU KULA DA SHI.

DAGA CIKIN HUKUNCE-HUKUNCEN AZUMI:

6. DAGA CIKIN AZUMIN AKWAI WANDA DOLE NE JERA SHI; KAMAR YIN AZUMIN WATAN RAMADANA, AZUMTAR TUBA DON KISAN GANGANCI, AZUMIN KAFFARAR ZIHARI, DA AZUMIN TUBAN YIN JIMA`I DA RANA A WATAB RAMADAN DA SAURANSU. KUMA DAGA CIKIN AZUMIN DA BA LALLAI BA NE JERA SHI AKWAI: RAMUWAR AZUMIN WATAN RAMADAN, DA AZUMTAR KWANAKI GOMA GA WADANDA BA SU SAMI HADAYA BA DA SAURANSU.

7. AZUMIN NAFILA YANA DORA WATA TAWAYA DA TA FARU A CIKIN AZUMIN FARILLA.

8. HANI YA ZO AKAN KEBANCE RANAR JUMA'A DA AZUMI, DA YIN AZUMIN ASABAR A LOKACIN DA BANA FARILLA BA, DA YIN AZUMIN KULLUM-KULLUM, DA KUMA YIN YIN TAZARCE A AZUMI, KUMA HARAMUN NE AZUMTAR RANAKUN IDI GUDA BIYU, DA KUMA KWANAKIN YANYANE